Gwamnatin Tarayyan Nijeriya

# MANUFA KAN HALAYYAR DA'A AIKATA GASKIYA DA RIKON AMANA TA KASA

## DABIN HAUSA

Office of the Secretary to the Government of the Federation (OSGF)
Independent Corrupt Practices and Other Related Offences Commission (ICPC)
and
National Orientation Agency (NOA)

OFISHIN SAKATAREN GWAMNATIN TARAYYA (OSGF)

HUKUMAR YAKI DA CIN HANCI DA RASHAWA

HUKUMAR GANGAMI DA WAYAR DA KAN JAMA'A

# MANUFA KAN HALAYYAR DA'A, AIKATA GASKIYA DA RIKON AMANA TA KASA

## DABIN HAUSA

© Copyright ICPC 2021

*All rights reserved. No part of this publication may be reproduced or transmitted in any form or by any means, electronic or mechanical, including photocopying or otherwise or stored in any retrieval system of any nature, without the written permission of the copyright holder.*

**ISBN:978-978-990-583-6**

Independent Corrupt Practices and Other Related Offences Commission
Plot 802 constitution Avenue,
Zone A9, Central Area,
Abuja.
www.icpc.gov.ng

Independence Corrupt Practices and Other Related Offences Commission was established in 2000 by Act No. 5 of year 2000. Its mandates include enforcement, prevention, public education and enlightenment

# ABUBUWAN DA CIKI



SAMUWAR MANUFAR.................................................... iv

Babi na Daya

GABATARWA................................................................. 1

Babi na Biyu

MUHIMMAN DABI'UN DA
MANUFAR TA KUNSA................................................... 3

Babi na Uku

AIWATAR DA MANUFAR................................................ 8

Babi na Hudu

KAMMALAWA............................................................... 10

ATUNTUBI OSGF/ICPC/NOA........................................ 11

## SAMUWAR MANUFAR



Hukumar yaki da cin hanci da rashawa (ICPC) ta samar da wannan saukakakken dab'i a kan manufa kan halayya da aikata gaskiya, da'a da rikon amana ta kasa tare da hadin gwiwar hukumar gangami da wayar da kan jama'a ta kasa (NOA) a matsayin wani bangare na kokarin sanya gama-garin yan Najeriya su yi cikakkiyar fahinta a kan wannan takarda ta manufa tare da tabbatar da mallakar ta da aikata abin da takardar ta kunsa.

Wannan dab'i ba zai maye gurbin takardar manufa ta farko wadda majalisar zartarwa ta tarayya (FEC) ta amince da ita a ranar 19 ga Agustan 2020 ba. Kuma shugaban kasa, Muhammadu Buhari ya kaddamar a ranar 28 ga Satumba, 2020 a yayin taron kasa na 2 a kan kawar da cin hanci a Gwamnati wanda a lokacin yayi daidai da lokacin da ake bikin cika shekaru 20 na hukumar ICPC. Ana sane wajen yin kokarin kewaye cikakkun bayanai na fasaha kamar cikakkun sunaye ko abubuwan da aka buga da tattaunawa a kan bayanai da kawo wuraren da aka sami dokoki da sauransu don a saukaka wa mai karatu fahimtar abubuwan da takardar ta kunsa.

# BABI NA AYA 1

## 1.0 GABATARWA

Hukumar yaki da cin hanci da rashawa (ICPC) tayi aiki tare da daidaikun mutane masu yawa da ma'aikatu a wajen samar da manufa kan halayya da aikata gaskiya da rikon amana ta kasa. Wannan ya biyo bayan illolin cutarwar cin hanci masu yawa a sassan gwamnati da na kamfanoni masu zaman kansu.

An yi wannan ne da nufin a taimaka wajen dawo wa wadannan sassa da martabarsu tare da ingata su a yayin inganta dabi'u da aikata gaskiya da rikon amana da shawo kan cin hanci a daukacin al'ummar Najeriya. ICPC tun da farko ta samar da manhajar nazarin dabi'u na kasa don koyar da dabi'u ga matasa 'yan Najeriya a makarantu. An tsara wannan manufa kan halayya da aikata gaskiya da rikon amana ta kasa a bisa muhimman abubuwan shirin don cusa kyawawan dabi'u ga al'umma.

## 1.0 MADOGARAR MANUFAR TA FUSKAR SHARI'A:

An samar da abubuwan da ke cikin wannan manufa daga dokoki kamar haka:

1) Dokar Sanin Makamar Aiki Bayani na 64 LFN 2004

5) Kundin Tsarin mulkin Tarayyar Jumhuriyar Najeriya na 1999 wanda aka yi masa gyaran fuska

2) Manufar ta kuma kunshi ra;ayoyi daga dabi'u na al'adu da na addinai na jama'ar Najeriya da dokoki na kungiyoyin kwararru kamar kungiyar 'Yan Jarida ta Najeriya da COREN da Majalisar yi wa Malamai Rajista ta Najeriya da sauransu




4) Dokar da'ar ma'aikata ta 2000

3) Taron wakilan Majalisar Dinkin Duniya a kan ya}i da cin hanci da sauran dokoki masu nasaba da wannan.

## 1:2 MUHIMMAN HANYOYIN MANUFAR:

Manufar ta wajabta wa dukkan 'yan Najeriya da duk wanda yake zaune a cikin Najeriya ko yake hulda da 'yan Najeriya da yayi alkawarin mara baya wa wadannan muhimman dabi'u na mutuncin dan'adam da fadin albarkacin baki da kishin kasa da sanin ya kamata da aikata gaskiya da rikon amana da hadinkan kasa da

kwarewar da ake sa ran gani daga kwararren ma'aikaci.

Hukumomin gwamnati a matakan tarayya da ta jihohi za su dauki matakin ladabtarwa idan aka yi wa wadannan tsare – tsare karan tsaye. Za a fassara hanyoyin manufar kafada da kafada da tanade-tanaden dokokin tarayya da na tsarin mulkin Najeriya da dokokin kungiyoyi na kwararrun da suke yin aiki da su da dokokin tafiyar da hukumomin gwamnati da kamfanoni masu zamankansu.

## 1.3 DALILANMANUFAR:

An tsara manufar ne don:

- Bunkasa kokari wajen inganta al'amura masu mamora na jama'arkasa da wadanda suke mu'amala da Najeriya da su rungumi, tare da yin aiki da muhimman dabi'un.
- A kubutar da kasa daga ci-gaba da gurbatar halayya da lalacewar dabi'u.
- A karfafa wa 'yan Najeriya gwiwar su sanya Najeriya gaba da komai. Yin haka zai taimaka wajen raunana cin hanci a matsayin dabarar tafiyar da rayuwa da tabbatar da dorewar rayuwar marasa karfi a yayin da ake takaita iko na masu karfi.
- Tsara hanyar da za a ci gaba da tattaunawa a kan yadda za a inganta dabi'u don 'yan Najeriya su kasance masu kyawawan dabi'u da dawo da martabar al'adunmu masu inganci.

# BABI NA BIYU 2

## 2.0 MUHIMMAN DABI'U DA MANUFAR TAKUNSA



## 2.1 MUTUNCIN DAN'ADAM



Manufar ta amince cewa, 'yan'adam suna da kimar da ba za a iya raba su da ita ba kuma lallai ne a daraja wannan kimar, kuma a guji yi wa wannan manufa karan-tsaye.

Bayanan wannan Dabi'a sun kunshi sashe na kundin tsarin mulkin Nageriya sashe na 2 kamar haka:

- Yancin rayuwa da 'yancin kai-komo da na magana da na yin taro da sauraren mutane daidai suke a gaban shari'a da sauraren shari'ar adalci da 'yancin fadar albarkacin baki da 'yancin kada a nuna masa bambanci da sauransu.

**Aiki da ita a aikace**:

- A sanya mutuncin Dan'adam agaba da ribar da zaa samu a aiki; lallai ne mutane su tofa albarkacin bakinsu game da yadda ake gudanar da ayyukan da suka shafe su; lallai ne mutane su sami 'yancin kadaicewa da na sirri. Haka kuma lallai ne su dauka ba za a amince da nuna kiyayya da aikata laifuka da firgita ko razana mutum don ya yi abin da wani yake so ba, da matsa lamba ga wani da yanayin aiki mai cutarwa da sauransu.

Fadin albarkacin baki yana nufin 'yancin ka ambaci ra'ayi da yin tasiri a matakin da za a dauka a yayin da tagazawa shi ne ka sanya hannu ko bada gudunmawa wajen aiwatar da wani aiki. Manufar tana karfafa gwiwar 'yancin mutane na fadar albarkacin baki da sanya hannu domin suma a dama dasu.

## 2.2 FADIN ALBARKACIN BAKI DA TAGAZAWA



Bayanan wannan Dabi'a sun Kunshi:

Tsarin dimokuradiyya da tafiyar da mulki bisa tsari da inganci don a yi koyi, da wakilci da rashin nuna bambanci dayin adalci wajen sauraren mutuum da sauransu.

**Aiki da ita a aikace**:

- Kowane mutun yana da 'yancin a wakilce shi a harkar tafiyar da gwamnati saboda ya ambata ra'ayoyinsa a kan yadda za a gudanar da mulki.
- Kowane mutum yana iya kai rahoton yin ba-daidai-ba ko yi wa wannan manufa ta halayya da aikata gaskiya da rikon amana karan-tsaye ga wata hukuma mai yaki da cin hanci da hukuma mai tilasta aiki da doka da kuma guje wa yin jawabi na kiyayya da yada labarin da ba a tabbatar da gaskiyarsa ba.

## 2.3 KISHIN KASA:



Kishin kasa yana nufin soyayya ga kasar mutum da kasancewa a shirye ko da yaushe don kare kasar. Kaunar kasa ya hada da alfahari da ita, yin biyayya da jajircewa don bada gudunmawa saboda kasa ta ci gaba. Rashin kishin kasa yana wanzar da dabi'ar da ba ta dace 'yan kasa su yi ta ba a game da abin da ya shafi kasarsu kuma kalubale na cin hanci da rashawa da rashin hakuri da kabilanci da sauransu suna kawo cikas wajen aiwatar da wadannan tsari na da'a, kishin kasa, gaskiya da rikon amana.

### Aiki da Kishin Kasa a Aikace

- Sanya tutar Najeriya da alama ta kasa a bainin jama'a da harabobin dukkan hukumomin gwamnati.
- Kasancewa dan kasa mai bin doka da kiyaye hakkokin al'umma da yin kalamai masu kyau a kan kasa.

## 2.4 SANIN YA KAMATA WAJEN MA'AMALA



Sanin ya kamata wajen aikata abubuwa na mutum na nuni da cewa, alhakin mutum ne ya taimaka wajen samun mafita ga kasa. Ana sa ran a koda yaushe 'yan Najeriya zasu nuna sanin ya kamata wajen ma'amalarsu.

Makasudan sanin ya kamata wajen aikata abubuwa sun kunshi:

- Inganta da'a da girmamawa da mayar da hankali a kan kyakkyawan aikin da ake yi da yin taka-tsantsan a yayin da wani al'amari ya bijiro a kasa.
- Bunkasa amincewa da sahihanci musamman a kamfanoni masu zaman kansu a wajen yin kayayyakin da zasu amfani al'uma da gudanar da ayyuka don su cimma matsayi mafi kankanta a kan tsarin samar da kayan da aka amince da shi a ksa da kasa da ke nuni da sanin ya kamata wajen yin kayayyaki ga masu amfani da kayayyakinsu da sauran masu ruwa da tsaki.
- Inganta yanayin wakilcin siyasa a tsakanin wadanda aka zaba  da jami'an gwamnati wadanda aka nada. Aiki da dabi'a a aikace: Nuna  sanin ya kamata da aikata gaskiya a wajen gudanar da ayyuka da hakkoki. Bayar da taimako ga halastattun hukumomin da suka kamata a wajen kula da bin doka da oda. Tsakani da Allah, mutum ya ambata kudaden da yake dasu ko yake samu ga hukumomin da suke tabbatar da bin dokar yin haka.

## 2.5 SANIN YA KAMATA WAJEN MA'AMALA



Aikata gaskiya da rikon amana na da ma'anar yin abin da yake tafiya kafada da kafada da tsare-tsaren da aka ambata ko tafiya bai daya da yadda ake son abu ya kasance da tsare-tsare da abubuwan da ake sa ran gani da imani mai sanya aiwatar da wani alkawari da aka yi. Aikata gaskiya da rikon amana na nuni da babu makawa yin abubuwa daidai don su tafi kafada da kafada dayin aiki da tsare-tsaren da aka amince da su da bukatun sanin ya kamata. Manufar tana karfafa wa 'yan Najeriya da mazauna ko bakin Najeriya gwiwar su rungumi aikata gaskiya da rikon amana ko babu wanda yake kallonsu domin Allah yana kallonsu aduk inda suke.

**Misalan Aikata Gaskiya da Rikon Amana a Aikace:**

- Gaskiya: Kasancewa mai aikata gaskiya da fitowa kai tsaye a yayin hulda dajuna ko a gwamnatance.
- Jarunta: Yin karfin hali a kan harkar da ta shafi jajircewa a wajen tafiyar da rayuwar mutum dayin abinda zai amfani jama'a da kasa ba tare da la'akari da kuncin da mutum zai gamu da shi ba.
- Duba kwazon kowa a kungiyance: Yin la'akari da cewa hakki yana kanka na game da duk abin da ka yi alkawari za kayi, ko kuma ka amsa duk wata tambayar da aka yi maka game da abin da ka yi ko baka yiba bisa gaskiya tsakanin ka da Allah.
- Tsoron Allah: Sanya tsoron Allah a matsayin jagora a wajen yin ma'amala da juna.
- Sauran sun hada da: Girmama juna da cika alkawari.

## 2.6 HADIN KAN KASA:



Najeriya kasa ce mai kabilu 250 da manyan addinai 2 da sama da harsuna 500. Yana da muhimmanci ga dukkan kabilu su kasance tunanin su guda ne kuma masu alaka da juna sannan masu hadin kai a matsayin kasa daya, al'uma daya.

Saboda haka hadin kan kasa na nufin tunanin Najeriya guda ce a matsayin kasa da kasancewa a kasar da dukkan jama'arta daidai-wa-daida suke ba tare da la'akari da kabilanci, bangaranci ko

banbancin addini ba.

Makasudan wannan dabi'a su ne a kirkiri sanya dukkan 'yan kasa su dauki kansu a matsayin tsintsiya daya su gamsu a kullum cewa za a gabatar da dukkan bukatunsu a harkokin kasa musamman saboda suna da 'yanci da ikon su zabi wakilansu.

**Hadin Kan Kasa a Aikace**:
Lallai ne dukkan jama'ar kasa su tabbartar da hadin kan kasa kuma su hada kai don aiwatar da abin da zai ciyar da kasar su da al'ummar su gaba; su guje wa rigingimu kuma su yi hakuri da juna a yayin ma'amala da junansu.

**Hujja da Hukunci**:
Lallai za a dauki matakin hukunta duk wanda ya saba waddanan dokoki.

## 2.7 KWAREWAR DA AKE SA RAN GANI DAGA KWARARREN MA'AIKACI:



Kwarewar da ake sa ran gani daga kwararren ma'aikaci tana nufin kyakkyawan ayyukan da ake sa ran gani daga mutumin da aka koyar da shi yadda ya kamata a kan wani aiki. Tana kuma nufin mayar da hankali a kan ganin samuwar aiki mai inganci tare da aiki da tsare-tsaren da aka shimfida da dokokin da suka danganci wata sana'a.

**Tushen Shari'a:**
Wadannan sun hada da dokokin aikin gwamnati da dokar da'ar jami'an gwamnati da dokokin aiki na kwararru da sauransu.

**Makasudi**:
Domin a samu da inganci a wajen gudanar da aiki

**Nuna Kwarewa A Aikace:**
Manufar ta bukaci cewa, lallai ne kwararru a gwamnati da yankasuwa masu zaman kansu su bayyana yadda suka tafiyar da aiki kuma su nisanci son zuciya da zai sanya su jayayya da juna. Kuma lallai ne kada su nemi ko su karbi nau'o'in kyaututtuka a yayin gudanar da aikinsu na gwamnati ko na kamfani sai fa nau'o'in kyaututtukan da musamman aka amince a karba. Ana sa ran ganin kyakkyawan ma'amala da kwarewa daga 'yan Najeriya da duk wanda yake yin harka da 'yan Najeriya a yayin gudanar da ayyukansa.

# BABI NA UKU 3

## AIWATAR DA MANUFAR

### 3.1 TSARA LOKACI DA AIWATAR DA SHIRIN AIKI



An shirya aiwatar da manufar ce ta bin mataki kashi-kashi da suka hada da:

- Taron bita tsakanin masu ruwa da tsaki a kan lamarin.
- Tsara shirin aiki da samfurin gudanarwa da za a yi amfani da shi wajen samar da misalai:
- Karkasa manufar zuwa matakai na kasa, jihohi da kananan hukumomi
- Yin gyara a kai-a kai da sanya ido da auna nasarar da akasamu.

### 3.2 SANYA AIKI DA DOKOKIN DA HUKUNCE- HUKUNCE



Hukumar yaki da cin hanci da rashawa (ICPC) da sauran hukumomin tabbatar da aiki da doka suna iya yin hukunci da gurfanar da duk wanda ya ki aiki da tsare-tsare da dabi'un da ke cikin wannan manufa kan halayya da aikata gaskiya da rikon amana ta kasa ko ya kasa aiwatar da umurninta.

Ana iya amfani da manufar wajen bidan hakki da menan adalci daga wajen hukumomi.

## 3.3 DOREWAR MANUFAR



Ana karfafa wa gwamnati da yan kasuwa ko kamfanoni masu zaman kansu a matakin tarayya, jihohi da kananan hukumomi gwiwar su yi aiki da Manufar da tsare-tsarenta.

Haka kuma za a yi amfani da wannan manufa a wajen tattaunawar yarjejeniyoyin samar da kayayyaki da ta cinikayya da ta zamantakewa da tattalin arziki da ta al'adu da masana'antar
kirkire-kirkire da sauransu.

## 3.4 DAIDAITAWA



Ofishin Sakaren Gwannatin Tarayya, da Hukumar Yaki da Cin Hanci da Rashawa da Hukumar Gangami da Wayar da kan Jama'a za su daidaita aiwatar da wannan manufa a yayin da dukkan Ma'aikatu da sassa da hukumomi da ma'aikatu a jihohi da a matakan kananan hukumomi za su mara wa manufar baya.

# BABI NA HUDU 4



## KAMMALAWA

Samar da wannan manufa kan halayya, aikata gaskiya da rikon amana ta kasa da ICPC da abokan huldarta suka yi da amincewa a aiwatar da ita daga bisani na nuni da samun nasarar a-zo-a-gani akan kokarin da Najeriya ke yi na sake gina kasa da dawo da martabar al'adunmu na gaskiya da rikon amana cikin ma'amaloli ko a gwamnace ko hukumance. Wannan macufar ta shafi kowane dan kasa, da wanda ke zaune a kasar.

Haka kuma manufar zata sanya jama'ar Najeriya kan turbar yin aiki tukuru don raya kasa kuma zata karfafa masu gwiwar nuna dabi'a ta girmamawa da kauna a tsakanin al'umma.

A yayin aiki da wannan manufa, son kai da ta'annati da rashin hadin kai da rashin tafiyar da harkar gwamnati da kyau za su zama tarihi a yayin da Najeriya za ta yi alfaharin samun matsayin da ya kamace ta a tsakanin kasashe.

**A Tuntubi - OSGF**
Shehu Shagari Complex, Three Arms Zone, Abuja.
Phone: +234-803-600-1627
Email: info@osgf.gov.ng

# A TUNTUBI ICPC

CIBIYAR ICPC TA KASA
Plot 802, Constitution Avenue
Zone A9, Central Area, PMB 535, Garki, Abuja, Najeriya.
Za a iya tura rahotanni ta yanar gizon ICPC wato ICPC website: www.icpc.gov.ng ko ta email a info @icpc.gov.ng. ICPC tana kare lafiyar dukkan wadanda suka bayar darahotanni.
Haka kuma za ka iya samun ICPC ta wadannan lambobi kyauta:

- MTN: 0803 123-0280, 0803-123-0281,0803123-0282
- GLO: 0705-699-0190,0705-699-0191
- 0800-Kira-ICPC(0800-2255-4272)

A kalli ICPC a Talabijin:
SHIRIN: 'Corruption Must Go' a NTA Network/International ranar Laraba, 3:30 na yamma.

KAFAR SADA ZUMUNTA: Za a iya bibiyar ICPC ta wadannan kafafen sada zumunta:

| | |
|---|---|
| Facebook | www.facebook.com/ICPCnigeria1 |
| YouTube: | ICPCNIGERIA |
| Twitter: | @ICPC_PE |
| Instagram: | @ICPCNIGERIA |
| Mobile App: | WahalaDay' a Android da Windows da IOSPhones |

# A TUNTUBI NOA

## CIBIYA:


Block B, Ginin Federal Secretariat Complex Area 1,
Garki Abuja, Nigeria PMB 27

Ofisoshi a jihohi 36 na Tarayya da Yankunan
Kananan Hukumomi 774

| | |
|---|---|
| KiraaLamba: | +234-803-592-8774 |
| E-Mail: | admin@noa.gov.ng |
| Website: | www.noa.gov.ng |
| Facebook: | www.facebook.com/ nationalorientationsgencynigeria |
| Twitter: | @noa_nigeria |
| Instagram: | @noa-nigeria |



**Re-printed and Simplified by:**
Independent Corrupt Practices and Other Related Offences Commission (ICPC)
National Orientation Agency (NOA)
March, 2021




TOGETHER